👻👻 AKWATIN MUTUWA👻👻

☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION☀️

FCWA

☀️home of qualities and trusted writers of the nation☀️

~Assalamu Alaikum~
~Gani na dawo maku da wani sabon littafi ina fatar yanda na fara lafiya Allah Ya bani ikon gamawa lafiya~

*Wannan shafin sadaukarwa ne gareku masoyana duk inda kuke*
*Ina sonku sosai*❤❤

*Page 1_5*

Wata mata ce zaune cikin daki wacce baza ta wuce shekara 35 a duniya ba,kana ganinta kaga mai ciki saboda yanayin zaman da tayi. Tabarma ce ta shimfida take zaune sama

Cikin yayi girman haihuwar yau ko gobe,tagumi ta buga kuma da ka kalli fuskarta kasan tana cikin damuwa.  Numfashi ta saukar mai sauti sannan ta fara magana "oh ni hajara tunda na samu cikin nan kullum cikin faduwar gaba da zullumi nake na rasa gane menene,duk da ban taba haihuwa ba nasan dai ba haka masu ciki suke ji ba gashi ina ji kamar wani mummunan abu zai faru da zuri'arta amma koma menene zan barwa zuciyata in dage da addu'a dan nasan kona fada ma yaya umar ba yadda zai yi ba"

Tana cikin zancen sai ga wani mutum ya shigo shekarunsa zasuyi 41,fari ne sannan yana da tsawo. Ko sallama baiyi ba haka nan ya fado cikin dakin kamar wani bijimin sa Wanda inda sabo hajaru ta saba da wannan dabi'a ta mijinta. "Yaya sannu da zuwa" yauwa kanwata ya jikinki da zaman kadaici? To yaya jiki kam Alhamdulillah sannan zaman kadaici ai har na saba shekara kusan goma fa kenan muke nan to wane  kadaici zanji" hakane kanwata wlh naga nawar inga kin haihu lafiya sannan abunda zaki haifa ma haka kinsa ina son yara yanzu tunda da bana zubar miki da ciki yanzu kila diyanmu sunkai biyar ko ya kare zancen da dariya

Hmm yaya kenan Allah dai Ya saukeni lafiya ; bai amsa mata ba wanda dama tasan hakan zata faru duk wata addu'a da zata yi indai kusa da yaya umar ne bazai taba amsawa ba shi kullum

burinshi yaci ya kwanta ibadar ma ba wani damunshi tayi ba sai idan hajara ta matsa sannan yayi wani lokacin ma ba yayi.

Maganarshi ta dawo da ita tunanin da takeyi " kinyi abinci yau da a'a ta amsa yaya kafa San yanda nake fama da jikina yau lafiya gobe ciwo kuma duk nayi maka magana muje asibiti baka taba yadda bansan me yasa ka kawoni wannan mugun dajin ka ajiyeni ba ka rabani da kowa daga Kai saini sannan Kai dinma fita kakeyi ka barni kamar wata mayya.........dallah rufe mani baki wannan maganar da tana tsiro da tayi ga jikinki wai me yasa kin cika mitar tsiya ne sau nawa zan fada maki ba wanda ya isa ya sakani fita dajin nan idan ba nine naso ba amma kullum sai kin dameni da zance to wlh ki kiyayeni ko dan kinga cikin ki ya girma na daina dukanki ne kawai Dan yanzu ina son ganin kwai na duniyar nan amma da ba haka ba wlh yau na lahira sai ya fiki jin dadi wawuya kawai" Yana gama fadar haka ya mike yayi hanyar dakin shi ya bar hajara zaune tana sharar hawaye. Itama da taga kukan bazai tsinana mata komai ba face ciwon zuciya Wanda take sa ran tana ma dashi tunda wani lokacin idan zuciyar ta na bugawa sai taji kila da akwai wani kusa da yaji sautin,mikewa tayi da kyar dan cikin yayi nauyi sosai ta wuce daki dan ta kwanta itama.

××××××××××××××××

Wasu mashaya ne guda biyu keta tambele cikin wani daji da ganinsu kasan mugun sha sukayi,surutu sukeyi maras kan gado. Dayan ne yace yaa baaba ni wlh talaucin nan ya isheni fa kullum idan zan kwalbe sai nayi sata sannan nake samu ; Wanda aka kira da baaba yace "kana ji ba gaye wlh gwanda kai tunda saika samo sannan kake bani nima fatana kawai Allah Ya kawo wani naman daga sama sai mun mashi eyane wlh" dariya suka kwashe da ita sannan wanda aka kira da gaye yace bari in dan matsa daga cikin wurin cen inyi fitsari Dan nan mutane sunyi yawa kallo na zasuyi ni kuma bana son ana kallon tsiraicina" dariya suka saka sannan gaye ya fara tafiya yana kara shiga cikin daji Yana yan surutan shi na mashayi.

Tafiya yake tayi har yanzu ya kasa samun wurin da zai yi fitsarin. Iska ne ya taso yana daga ganyen dake nan kasa shidai gaye bai tsaya ba da tafiyarshi ba cen yaji yayi tuntube da wani abu kamar dutse; tsayawa yayi sannan yace "kaga tsinannun mutane wato duk da nazo nan inyi fitsarin Saida kuka biyoni ko to zan maka eyane wlh.

Har zai wuce sai yaga kamar akwati ne wajen dukawa yayi ya taba yaji dai shi ne dariya yayi yace sai ni tanimu gaye ashe dai labaran da nake karantawa da gaske ne wadan dake shiga daji suna samun akwatin kudi da gaske ne, ihu ya sakeyi sai ni tanimu gaye mai sa'a yau dole in kwana ina kwalbewa. Kokarin bude akwatin yayi amma ya kasa sabida wani kwado da akasa aka kulle; wani dutse ya gani kusa ya dauka ya fara bugun kwadon tun yana na marmari har ya fara gajiya da kyar dai ya samu ya balle akwatin budewa yayi yaga babu komai sai ƙwarangwal ja ba baya yayi Wanda yayi dai² da wata irin walkiya tare da wani iska mai firgitarwa da suka taso lokaci guda. Wata irin kara akayi mai firgitarwa sannan aka fashe da wani kuka Wanda amon shi ba dadin sauraro;wata irin halitta ce wadda idan ka kalla sau daya to baza kayi

marmarin kara kallawa ba, tanimu gaye naga iska ta dauke ta maka shi da bishiyar dake nan sannan aka jawo shi kamar kayan wanki aka dinga makawa kasa ihu yake yana kiran dan Allah kuyi hakuri ku kuke ganinmu bamu ke ganinku ba wlh na fasa son kudin ko giyar ma na daina sha sannan zan dinga gaida iya kullum kuyi hakuriii... shiru yayi sanadiyar wuyanshi da aka karya kum. Dariya ta kwashe dashi sannan ta fara magana "daga yau na fara farauta kuma babu Wanda ya isa ya dakatar dani shekarata dari cikin akwati yau gashi wani ya fitar dani hhhhhhhhhh,bat ta bace.

Wanda yayi dai² da wani faduwar gaba daya tsinkayi hajara dan tunda ta shiga daki ta kasa bacci sai tunani takeyi; iska taga yana kadawa tare da jin wani sautin kuka daga nesa.

Baaba ne tsaye sai zage² yake irin na yan shaye² yana wannan banzan daga fitsarin ne har yanzu bai dawo ba gashi dare yayi sosai har mutane sun fara watsewa (dariya nayi nace lallai kam baaba kana ruwa ko ina mutanen suke nan oho) tafiya ya fara yana idan ka dawo ka sameni gida nikam na gaji. Wani kare ya gani yana nufar inda yake da gudu gashi kana ganin idanunshi jajir dasu kamar an barbada mashi barkono ciki, baaba na ganin dai kare wajen shi yake zuwa ya fara tafiya da sauri yana hadawa da gudu ai kamar wucewar iska yaga kare gabanshi.

Baya ya fara ja yana fadin kada ka matsoni dan wlh zan maka eyane inaa kare bai San meya ke fada ba wata irin tsalle yayi sai gashi saman jikin malam baaba wata kara ya saki yana jama'a ku kawo dauki zai cijeni,wlh kada ka fara nace zan maka eyane fa. Wata cafka da karen yayi mashi kawai sai ga kan baaba cikin bakin kare,nan ya fadi ba kai jiki sai rawar disco yake kasa,bacewa Karen yayi sannan wurin yayi tsit kamar wucewar mutuwa..

××××××××××××××××

Koda safiya tayi da kyar hajara ta mike sabida ciwo da mararta keyi haka nan dai ta daure ta sauko saman gado sannan ta shiga bayi tayo alwala fitowa tayi ta shinfida abun sallah ta tayar da kyar take dukawa cen tana cikin sallar taji kamar an tureta faduwa tayi saman cikin wata kara ta saki nan take jini ya balle mata saiga haihuwa kuma gadan² ta fara nakuda cikin ikon mai sama ta haihu ihu ta sakeyi ko yaya umar zaiji tunda tasan bai kaida fita ba amma shiru babu shi ga jini sai malala yake kasa kamar ruwan wani teku.

Yan dabaru tayi ta yanke cibi nan ne taga ashe mace ta haifa' kurawa yarinyar idanu tayi tana jin tausayinta na shigar ta ga wani bakon al'amari da takeji ga jikinta,cikin minti biyar hajara tace ga garinku tana rike da yarinyar ta ga hannu da sai kuka takeyi.....

*Maryam H*

[10/15, 8:04 AM] Hayat: 👻👻 AKWATIN MUTUWA👻👻

☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION☀️

FCWA

☀️home of qualities and trusted writers of the nation☀️

*~WANNAN PAGE DIN NA SADAUKAR DASHI GA DAUKAKIN MASOYAN WANNAN LITTAFIN BANIDA BAKIN DA ZAN GODE MAKU AKAI SAI ADDU'AR ALLAH YA BAR ZUMUNCI DA KAUNA~*🥰🥰
~*INA YINKU OVER*~👌👌

*Page 11_15*

Tafiya sukeyi har suka zo bakin kofar shiga gidan tura kofar yayi ya shiga itama ta shiga,kujera ya nuna mata da ta zaune ya kawo mata ruwan da kai ta amsa mashi. Kicin yaje ya dauko kofi sannan ya dawo ya bude firiji ya dauko goran ruwa,inda take ya kawo mata ruwan godiya tayi sannan ta bude goran ruwa ta zuba tasha; Saida taji ta koshi sannan ta ajiye kofin magana ta farayi "bawan Allah na gode da taimakona da kayi dan da ban samu ruwan nan na nasha ba da bansan yanda zanyi ba" kai ya gyada mata sannan yace babu komai ai, ta buda baki da niyyar magana sai sukaji kukan jaririya cikin daki umar ya mike yace ina zuwa da sauri yayi cikin dakin dauko ta yayi yana jijjigawa alamar tayi shiru. Cen falo kuma bakuwa na gani ya bar wajen itama saita bace tana dariya

Bacewar ta yayi dai² da shigowar umar falon turus yayi na ganin ba kowa falon; magana yayi to ita wannan ko tafiyarta tayi taga ban fito ba. Zama yayi yana tunanin abun yi dan shifa yarinyar nan yake tausayawa ba wanka balle akai ga maganar abinci.

Gaskiya ya kamata ya kirasu ummah asan abunyi yanzu gashi gawar hajara ma ta bace baisan inda zai ganta ba sannan ga karin tashin hankalin abunda ya faru dashi lokacin da zai bar dajin

nan.

×××××××××××××××××××
Wani irin daji ne wanda ko cikin mafarki ka ganshi kasan mugun mafarki ne kayi. Wani katon akwati ne wajen duk ya tsufa alamun ya dade wajen gefe dashi kuma kawuna ne da gangar jiki na matattu har sun zama kwarangwal. Wata irin iska ce ta kada mai tsoratarwa baka ganin komai sai kura dake tashi sama dariya aka farayi sannan iskan ya fara ragewa,wata halitta ce ta fara bayyana ;farin kayane jikinta amma duk ya farke sannan gashin kanta wani iri dashi duk ya mike tsaye gashi kamar sayyun itatace,idanunta kalar ganye,bakinta kamar wani kofi sannan bata da hanci dan wurin shafe yake kamar anyi filista.

Wajen akwatin nan ta matsa hannu kawai ta daga sama tayi wata kwalamniyar magana saiga akwati ya bude, kwalamniyarta ta sakeyi saiga gawa ta fito ta fadi kasa,wata ta fito saida gawa uku ta fito daga akwatin sannan ya rufe. Ashe gawar su hajara ne dasu tanimu gaye.

Wani irin ihu tayi sannan ta fara magana cikin karaji "bazan taba sanya ba saina kashe kowa yanda kuka kashe ahalina sannan ni kuka sakani cikin wannan akwatin to dashi zan dinga farauta duk wani ahali dake doran kasa saina batar dashi" tana gama fadin haka ta bace batt..

××××××××××××××××××
Umar ne zaune ya rafka uban tagumi abun duniya ya ishe shi yaje da niyyar daukar waya ya kirasu ummah amma baiga wayar ba ashe tana cikin motarshi kuma gashi motar tayi batan dabo,yanzu tunaninshi yanda zai bar wannan gidan ya koma gari ko suna a sakawa yarinyar nan da itama daga zuwan ta duniya ta fara cin karo da bala'i. Tun dazu yake gwada fita cikin gidan amma ya kasa da yaje buda gate sai yaji kamar an dora wani gingimemen dutse wajen sannan sai ya dinga jin kamar muryar hajara na kiranshi

Yana cikin wannan tunanin ne yaji kamar silin dakin zai fado saboda wata irin jijjiga da yakeyi mikewa yayi da sauri ya dauki diyarshi ya riketa sosai sannan ya dawo falo ya tsaya; kofar falon aka bude cen saiga wani kwarangwal ya shigo falon wasu na biye dashi suna zuwa basu tsaya wata² ba guda ya cafke wuyan umar ya daga shi sama tari ya fara saboda azaba sannan ga yarinya hannunshi wanda idan yayi wasa tana fadowa. Suna cikin haka saiga wata halitta ta bayyana inda suke wani yare tayi saiga umar ya fado da kadan ya haye diyarshi su kuma kwarangwal suka koma baya.

*Bari mu koma wajen iyayensu umar*

×××××××××××××××××××

Ummah ce kema Abba magana akan yayi sauri suje su dibo yaran nan ko lafiya tunda umar bai zo ba kuma bai kira ba gashi wayarshi ko an kira kashe take, fitowa Abba yayi yana wlh Fatima kin cika mitar tsiya yanzu dai gani sai mu tafi ko. Fitowa sukayi suka shiga mota direba yaja mai gadi ya bude kofa suka fita. Tunda suka fito gaban ummah ke faduwa addu'a kawai takeyi har suka fara nusar cikin daji shi kanshi Abba wani iri yake ji dauriya kawai yake tare da addu'ar.

Sunyi tafiya mai nisa sannan suka zo gidansu umar Abba ya fita ya budewa direba kofa ya shigar da motar ciki, karasawa sukayi ummah ta fito aka bar direba cikin mota, ummah ke gaba har sukazo dab da bude kofar falo wanda yayi dai² da ihun da umar yayi sakamakon fatalwa ta caka mashi kumbarta ga wuya....

*Maryam H*
[10/16, 6:52 AM] Hayat: Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/L3K7SmNat3v1GNB8AxWxdJ

👻👻 AKWATIN MUTUWA👻👻

☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION ☀️

FCWA

☀️home of qualities and trusted writers of the nation ☀️

*Page 16_20*

Innalillahi wa inna ilaihi raji'un me nake gani haka cewar ummah da sauri fatalwar ta sake wuyanshi suka bace,fadowa yayi wanda jaririyar tayi gefe guda tare da tsallara wani kuka na azaba. Da gudu su Abba suka karaso inda suke ummah ta dauko jaririyar shi kuma Abba yayi wajen Umar daya sume tuni sabida azaba, kuka ummah ta fashe dashi tana fadin "wai menene haka nake gani ina ita Hajara din tabar yarinyar hannunshi sannan wace irin halitta ce wannan me kuka yi mata" ta karashe zancen tana kuka; Abba ne ya fita da sauri ya kira direba suka kama Umar suka kaishi cikin mota, dawowa yayi yace ummah ta tashi ta dibo Hajara tazo su bar gidan,koda ta duba bata ba dalilinta ko'ina an duba bata haka nan suka kama hanyar gida

ba Hajara amma kuma kowa da abunda yake sakawa cikin ransa.

Sun zo fita cikin dajin kawai suka ga mutum kamar an jeho shi daga sama,wani wawan burki direba yaja wanda saida Umar ya kusa fadowa daga kujerar da yake kai. Tasowa mutum yayi yana nufo su amma kuma baida kai gangar jiki kawai ne,ashe gawar baaba ce ai suna ganin haka Abba yace ma direba yayi sauri ya tayar da mota su bar wajen

Haka ko akayi yana tayarwa baaba na kawowa kusa dasu ji kawai sukayi ana "tunda kuka zo wajen nan yau saina maku eyane kun gane ai bazan bari ku bari wajen nan haka siddan ba tare da na maku eyane ba",da wani matsiyacin gudu direba ya bar wajen su kam su ummah ba abinda ake sai addu'a dan iya tsoro anji shi. Suna barin wajen baaba gaye ya kwashe da wata irin muguwar dariya sannan wata iska ta tashi tayi sama.

Koda suka kai gida baki daya jikinsu yayi lakwas kamar wadan da suke je filin daga aka kayar dasu,fitar da Umar sukayi aka shigar dashi gida ita kuma ummah daki taje ta dauko zani ta goye jaririya sannan ta fada kicin ta dora ruwan zafi saida suka tafashe sannan ta samo roba ta zube ruwan kadan ta surka sannan ta wanke jaririyar tas,Allah Sarki yarinya taji ruwan zafi har wani kulle idanu take alamun dadi. Kaya aka canja mata lokacin Abba ya fita ya siyo madara aka dama mata sannan aka sa mata a baki,tana kamawa kam ta dinga tsotsa "saida tayi nak sannan ta saki ta bingire da bacci.

Wasa$^2$ saida Umar ya kwashe kwana uku baisan duniyar daya dosa ba a kwana na ukun ne ya farfado yana bude ido ya kafta wata irin ihu da ta kusan saka ummah sakin jaririya da take ba madara, da gudun ceton rai ta fada dakin saiga Abba shima yaji ashe. Suna zuwa suka iske shi sai fizge$^2$ yake yana "kada ku kasheni dan Allah kuma ku dawo mani da gawar matata wlh koda ta mutu ina sonta" da sauri Abba ya matsa kusa dashi ya fara tofa mashi addu'a ita kuma ummah har ta bare baki ta fara kuka tana "yanzu badai hajara ta mutu ba to kuma ina gawar waya....." wani kallo da Abba yai mata yasa ta yin shiru ba tare da ta karashe maganar ba. Cikin ikon *mai sama* Umar ya bar fizge$^2$n da yake sannan ya rage surutun ma haka nan bacci ya dauke shi, saida suka ga haka sannan suka baro dakin falo suka dawo suka zauna sannan Abba yace "na rasa gane wani irin tunani ne kuke dashi mata wlh ace kinga mutum ya farka cikin yanayi amma wasu tambayoyin rashin kai kike mashi ai kya bari ya dawo hankalin shi duka sannan mu tambayeshi meke faruwa,Ni tsoro na ma idan ba wajen daukar maganar shi ya yaje ya jawo aljanu ba gashi kuma yace su dawo mashi da gawar mata wanda haka na nufin hajara ta mutu shi ne kuma suka dauke gawar.lallai ya zama dole mu tashi tsaye da addu'a sannan wannan jaririyar gobe za'a yanka mata rago asa mata sunan mahaifiyarta"" da to kawai ummah ta amsa sai sharar kwalla take...

××××××××××××××××××××××××××
Wani saurayi ne zaune cikin dakinshi da yasha mai da yaji na kayan alatun duniya idan kaga dakin zaka rantse baza'a mutu ba,kwalaben giya ne gaban shi sai kwalbewa yake abunshi daya shanye wannan sai ya ture kwalbar gefe yaja wata. Yana cikin wannan yanayin ne yaga kamar mace na mashi gizo tun yana tunanin ko giyar da yasha ne ta fara aikinta yaga dai ba haka bane

Kallo ya kare mata iya haduwa ta hadu kamar ita tayi kanta don kyau kusa dashi tazo ta zaune sannan ta fara magana kamar mai rada cikin wata iriyar murya mai saka mutum fara jin baccin dole "haba salim me yasa kullum baka gajiya da shan giya ne eyen to nidai yanzu ka tashi muje ka rakani shan ice cream" kamar wanda aka dorawa wani magana disu haka yaji gashi shi dai baya son zuwa tunda bai san ko wacece ita ba kawai cikin dakinshi ta bayyana sannan tana wani ya kaita tasha ice cream shida ya riga ya dawo gida sai gobe zai fita kuma,amma kuma baya iya musa mata. Haka nan ya mike suka fita daga dakinshi na bacci zuwa falo kamar rakumi da akala.

Falon ya hadu karshe kamar ba duniya ba, haka suka fito suka shiga mota mai gadi ya wangale masu gate yana ranka ya dade sai ina baiko kalli inda yake ba yasa Kai ya bar gidan; tabe baki mai gadin yayi yana Allah dai ya shirya ace yaro kamar dangin maguzawa yanzu kullum sai yayi tatil zai dawo ma gida kuma iyayenshi babu Wanda ya damu da halin da kake ciki su ganinsu burgewa ce,yanzu ko Ina yayi shi kadai haka cikin daren nan oho(ido na zare shin mai gadi baka ga su biyu suka fita kake Kiran shi kadai,to ina bakuwar tashi ta labe da har mai gadin ya kasa ganin ta)surutan shi ya gama sannan ya kulle gate din ya koma dakinshi ya kwanta.

*Waye Salim*

Salim shazali shi ne sunanshi da ga Alh shazili Muhammad hamshakin mai kudi dake garin kano,sana'ar saida gwala gwalai yake yana da shaguna kusan uku a garin kano sannan da wasu dake kasar amurika duk na gwala gwalai, Yana da mata hajiya falmata kanwar abonkin shi ce dake maiduguri ya aura. Salim shi kadai Allah Ya basu Wanda dalilin haka suka nuna mashi gata na kazanta,tun daga secondary har University a amurika yayi wanda sanadiyar haka ya kara samun lasisin lalacewa.Ba abinda Salim baya yi na assha shi ne shan giya,neman mata da dai sauran miyagun dabi'u sannan duk abinda yayi wajen iyayenshi dai² ne basu taba yi mashi fada ba,aya guda wannan ta qur'ani bai sani ba amma waka ko wani tsami yayi ta to yasan da zaman wannan waka..

*Ci gaban labari*
Koda suka fito gida tambayar ta yayi inda zasu je ce mashi tayi su ci gaba da tafiya idan sun kawo wajen zata mishi magana,haka ya dinga sharara gudu saman titi kamar wani dan tseren mota. Sunyi nisa sosai dan har sun fara fita cikin gari wani daji tace ya tsaya; tsayawa yayi dan

ji yake kamar *konturolin* dinshi take.

Koda suka tsaya cewa tayi ya fito ya biyota; fitowa yayi yana binta da baya har suka zo wajen wani tafki , shiga tayi shima Salim ya shiga tafiya suke yi har sukazo tsakiyar ruwan hannu tasa ta jawoshi ta tura kanshi cikin ruwan

Wutsil² ya fara yi da hannunshi tun yana yi da karfi har jikinshi ya saki alamar dai rai yayi halinsa( mudai sai muce Allah Ya jikan rai su salim anyi zuwan zomo kasuwa yazo da gudu ya fita da gudu. Tunda aka haifeka baka taba tsinana komai mai kyau ba sannan aikinka na karshe ma marar kyau gashi ka tafi inda ba'a dawowa. Mudai fatar mu Allah Yasa mu cika da imani sannan mu mutu muna aikata alkhairi. Amin)

Tana ganin ya mutu tayo wata sufa ta fito daga ruwan girgiza tayi sai gata ta koma sak Salim,dariya tayi sannan tace saura iyayenka. Mota ta tayar tayi hanyar gidansu Salim ,Koda taje mai gadi harya fara bacci odar da ta dinga yine ya tadashi da sauri ya fito ya bude gate din Yana Allah wadai da halin Salim Dana iyayenshi.

Saida ta shigar da motar sannan tayi sashen iyayen su kuma lokacin har sun lula duniyar sama jannatin bacci .tana shiga ta girgiza sai gashi ta dawo wata halitta mai tsoron kallo

Kwalamniyarta tayi kawai saiga gida ya fara kamawa da wuta ,Saida tayi dariyar muguntar ta sannan ta bace

Su Alh shazali da Hajiya falmata an bude saleba sai kwasar bacci ake ana minshari kamar wasu shanu da suka ci dussa suka kasa tashi. Cikn bacci hajiya falmata ta fara jin hayaki kamar ana shakar wuyanta da sauri ta tashi ta fara bubbuga mijinta tana Alh tashi kamar wuta fa keci. Magagin bacci ya fara Yana "dan Allah falmata ki kyaleni inyi bacci na gaj.....bai karasa zancen ba yaji wani duka da takai mashi aiba shiri ya mike hanyar fita dakin sukayi suka kama jan kofa amma taki budewa wajen wayar tarho ya koma ya danna lambofin *faya sabis* suna dauka yace "nine shazali mai gwala gwalai kuzo gidana wuta ta kama... Bai karashe zancen ba aka jeho wani harshen wuta Wanda yayi sanadin shi nan take itama falmata tashin hankalin abunda ta gani yasa zuciya ta buga nan take ta zube kasa mace.

Mai gadi ne yaji kuwwar motar yan *faya sabis* da gudu ya tashi ya bude kofa sai sannan ya hango yanda wuta ke ci,bude kofar yayi suka shigo binsu yayi da gudu har suka Kai wajen kofar shiga gidan. Ruwan aka fara watsawa amma kamar ba'a watsa komai Saida kusan mota uku tazo sannan wutar ta tsaya, da kyar aka gano gawarsu su Alh shazali.

Lokacin gari yayi haske mutane har sun fara taruwa . gawar ba kyan gani sabida soyewar da tayi

Danginsu aka kira sukazo aka basu gawar su sukai masu sutura akai kaisu gidan gaskiya inda babu Wanda bazai je ba.

Anyi bincike an rasa gano mai ya jawo gobarar aka watsar da *kes* din aka raba gado dingi suka dinga bushasha.......

👻👻 AKWATIN MUTUWA👻👻

☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION ☀️

FCWA

☀️home of qualities and trusted writers of the nation ☀️

*Page 26_30*

Sai kusan shida na safe ta tashi wanka tayo tare da alwala tayi sallah,shiryawa tayi cikin kayan makaranta yadin riga da siket kalan kwai sai hijabi karami kalan anta. Falo tazo lokacin bakwai da rabi ta kusa abinci taci agurguje sannan ta fito wajen gate dan ko ummah basu hadu ba dama ta saba sai ta dawo daga makaranta suke haduwa ita ummah'r na cen tana gag gabar bacci.

Tunda ta shiga mota direba ya fara tafiya take jin wani iri ga jikinta gashi sai taji kamar ana mata rada cikin kunne, sannan ita ba wani ma'abuciyar addu'a bace duk da tana zuwa islamiyya karatun ba wani dagata yayi ba tafi bama boko mahimmanci gashi tana da kokarinta gwargwado tunda ita ke yin na daya tun tana firamare har yanzu da ta shiga sakandare aji biyu sannan su iyayen nata ba wani kwaba ta suke ba komai taga dama shi takeyi a ganinsu tunda ta rasa uwa baza tayi maraici ba,Abba ma ne ke tsawatarwa wani sa'in idan yaga abin yayi yawa.

Suna zuwa cikin makarantar direba ya tsaya ta sauka magana yake "masu gida Allah Ya bada Sa'a" wani juyowa da tayi shidai direba gani yayi kamar ba ita ba dan rabin fuskar ta a daye sannan rabin ba ido daya; da gudun ceton rai ya figi motar yayi gaba.

Koda ta shiga aji babu wanda tayiwa magana duk da tana da fara'a amma yau kam fuskar nan kamar kunun dare, kujera ta zauna ba tare da ta kalli kowa ba

Wani yaro ne dan kasada mai suna Abbas dake gaban kujerar ta ya juwa yana " wai ke yau meya sameki kikewa mutane kamar kina jin warinsu" har ya gama zancenshi bata ce komai ba,koda malamai suka shiga sunga canji wajen ta sabida taki magana da kowa. Har saida aka tashi sannan tacewa Abbas ya tsaya zata ganshi bai kawo komai ba yace to,saida kowa ya watse sannan Hajara ta mike ta dawo gaban Abbas irin fuskar da tayiwa direba tayi mashi wani wuntslawa yayi da baya daya fadi hannu ta mike sai gashi yayi dogo bata tsaya wata² ba ta caka masa kumbar ta wuya tun yana ihun neman taimako har dai ya kasa gashi ajinsu shine kusan karshe ba'a jin komai,zuwa cen jiki ya saki bacewa sukayi sai cikin wannan mugun dajin,cikin akwatin nan ta jefashi sannan ta bace. Bakin gate din makarantar su ta bayyana bata dade ba saiga daddy'nta yazo dan direba ya sheme yace alan baran baida lafiya don gudu yake ya koma ya kara cin karo da wannan fuskar tata kamar fatalwa. Koda yazo shi kanshi yasha mamakin ganin yanda ta hade girar sama data kasa sai harde fuska take,shiga motar tayi ba tare da tace kala ba saida suka fara tafiya sannan ya fara magana"haba baby'n daddy meya faru kika kyalleni ne? Ko inda yake bata kalla ba bare yasa ran samun amsa da yaga taki magana ya kyalleta

Suna zuwa gida ta buda mota ta fita ciki ta shiga ba tare da tawa kowa magana ba tana shiga dakin ta ta fada kan gado ta fashe da wani kuka mai sautin ganga cikin kukan take magana " badai kun kashe mu ba to nima saina ga bayanku.

*Wacece wannan fatalwa*

A'ishatu  ibrahima ne sunanta su yan asalin jamhuriyar Nijar ne cikin garin agadaz su uku suke ga mahaifinsu itace babba sai Usmanu da kanensu Yusufu. Ahali ne masu burgewa,mahaifinsu ibrahima Yusufu su goma ya haifa amma shi kadai yake ga mamarshi bayan haihuwar shi da awanni tace ga garinku sanadiyyar tsafin da akayi mata na turo mata bakaken aljanu,shi ne karami sai yayunshi Abubakar,jimirau,auwalu,fatsima,mulaika,Sulemani,zuwaira,halimatu da Idirisa; sun taso cikin kiyayyar dan uwansu wanda ammah wato mahaifiyarsu ta dasa masu.

Amma wata irin mushrika ce wadda ko cikin jahilan farko sai an tono irinta tun farkon da Yusufu zai yi aure taso hanawa amma tsafin bai ci ba saida zainaba ta shigo gidan wato uwar ibrahima Sannan ta ci gaba da kulle kullenta har ta samu ciki wanda hankalin ta ya tashi taje wajen bokanta aburu kukuma tace tana so akashe zainaba kafin ta haihu yace bazai yiyu ba sedai idan ta haihu; shi ne bayan ta haihu aka turo mata aljanu suka shaketa ta mutu.

Tunda ibrahima ya tashi yake cikin gararin rayuwar babanshi dai ke raga mashi kuma sai Allah Ya albarkaci hannunshi komai ya rika sai yayi albarka,har dai yayi aure yana cikin ukuba wanda wannan lokacin kuma babansu ya rasu yayi kukan rashi daga baya ya dangana

Ibrahima nada kudi sosai wanda shi ya kara tursasa hassada ga yan uwanshi kullum cikin neman hanyar cutar shi sukeyi.

A'ishatu yarinya ce mai masifar tsiya idanunta tsaye suke bata da kunya ko kadan iyayenta kawai take dagawa kafa sai kanninta.

Ranar babansu na zaune cikin gida yana hutawa saiga sulaimani yazo wai su hada aure tsakanin diyansu wanda ko babu komai zumunci zai karu da jin haka ibrahima yace sam bazai bama dan shaye$^2$ diyarshi ba kawai su nemi wata, wannan furici yayiwa sulaimani ciwo wanda har yakai saida suka hada taro da yan dakinsu duka inda akace zasuje wajen boka aburu kukuma sai asan abunyi; sunje ya basu wani magani da idan suka shiga gidan komai zasu iya yi babu wanda zai hana su sannan da zarar sun hadu da ibrahima su barbada maganin ga wuka su caka masa ga zuciya.

Saida dare yayi sannan sulaimani, Idirisa suka shirya tare da dan dan sulaimani mai suna jibirila, gidan sukaje inda babu wanda ya gansu

Dakin baccinsu suka nufa suka tadosu suka taso keyarsu zuwa falon gidan sannan suka tado da yaran koda sukazo, sulaimani bai tsaya wata$^2$ ba ya caka masa wukar saitin zuciya sannan duk suka yanke sauran saura A'ishatu tana ganin haka ta fara ihu amma babu wanda zai ji wani akwati ne da sukazo dashi suka jawota suka turata ciki tana ta ihu amma babu wanda ya kula ta sannan suka saka kwado suka datse

Cikin daren nan suka kama hanyar wani daji mai abubuwan tsoro suka gefar dashi,wanda wasu mutane suka shiga dajin suka ci karo dashi suka dauka a tunaninsu kudi ne sunyi tafiya mai nisa har suka shigo najeriya sunyi bakin kokarin bude akwatin amma sun kasa shine suka yadda shi inda tanimu gaye ya gani har ya samu sa'ar budewa...

*Ci gaban labari*

*Maryam H*

*Maryam H*

🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇🍇

*SHU'UMIN NAMIJI !!*

*Written by*
phatymasardauna
*🎈Mrs Sardauna🎈*

*Dedicated To My Lovely Brother Khabeer*

*🌈KAINUWA WRITERS ASSOCIATION*

*https://www.facebook.com/kainuwawritersassociation*

*WATTPAD*
@fatymasardauna

*Editing is not allowed 📵*

*Chapter 12*

*( INA MAI BAKU HAKURI DOMIN KUWA KWANA BIYU, ZAKUJINI SHIRU BA NEW UPDATE, WATA ƘILA NAYI 1 WEEK BANYI TYPING BA, WATAƘILA KUMA BAZAN KAI HAKANBA, HAKAN YAFARU NE SABODA WANI DALILI NAWA, INSHA ALLAH AMMA ZAKUCI GABA DA JINA IDAN KOMAI YA DAI DAI TA, NAGODE....)*

*Kuɗanyi manage da wannan 👇🏼*

Kasa ƙare maganar Baffa yayi sakamakon tozali da kuɗaɗen dake gaban Inna da yayi,   cike da tuhuma yake kallon Inna yamakasa ce da'ita komai,  ganin haka yasa Inna ta washe baki, haɗe da soma tattare maƙudan  kuɗaɗen, cikin hanzari Baffa yasanya hannayensa duka biyu ya wawashi kuɗin, haɗe da cusawa cikin aljihunsa, da sauri Inna tayo kansa tana muzurai, haɗe da cewa "Haba Malam yazakayi haka, aidai katsaya nayi maka bayani kafun ka kwasa rabonka ko" harara Baffa ya watsamawa Inna haɗe da taɓe baki yace " ba abun da bansani ba, nasan

duk wani abu dakike shiryawa,  kuma wallahi daga yau idan aka sake kawo kuɗi cikin gidannan ba ki jira dawowata munraba ba, ninasan matakin da zan ɗauka, yarinyace dai ƴar wa na ne, don haka babu wanda ya'isa ya gwadamin iko da'ita, kuma shima saurayin  zaizo yasameni haka ake zuwa hira babu wani tambayar izini ba komai" Baffa yaƙare maganar yana mai nufar ƙofar fita daga gidan, yana fita Inna ta buga tsuka haɗe da cewa " shikenan kuma ae tunda yagano abun danake shiryawa, bazai taɓa barina naci arziki ni ɗaya ba, mcheeew !" taƙare maganar tana mai tattare ƴan ragowan kuɗaɗen da Baffa ya bar mata,  raba snacks ɗin biyu tayi taɗauki rabi, yayinda tabarmawa Zahrah rabi, waya kuwa danƙamawa Zahrah abunta tayi, domin ita keypad ma bawani iyata tayi ba, balle kuma shafa shafa (touching screen)...  Jigum haka Zahrah tayi zuciyarta cunkushe take da tarin tunani kala kala,  da zaran ta kulle idanunta, mood ɗinsu na ɗazu ne ke faɗo mata, wanda hakan yasanya takejin gaba ɗaya jikinta yayi sanyi, batasan dame zata ƙira wannan yanayinba, saboda batasan ma da akwaishi acikin duniyar nan ba, duk dacewa bawani abune yashiga tsakaninsu ba, amma kusancin da sukayi da juna duk ya dagula mata lissafi, ga fitinannen ƙamshin turarensa daya kama jikinta, tamkar wacce tayi wanka da turaren,daga wani ɓangare na zuci yarta kuwa kaico takeyi da mummunan hali irin na Inna da Baffa, wato su baruwansu da koma waye zaizo wajenta, sudai kawai abasu kuɗi  suka sani, koda ma iskanci takeyi su baidame su ba kuɗi kawai suke so, haƙiƙa rashin iyaye babban matsalane arayuwar ƴa mace musamman  ma idan batayi dace da iyayen riƙo nagari ba, sai kuga rayuwarta nashirin lalacewa, akan abun da bai kai yakawo ba, Allah ka zama gatan mu aduk inda muke Ameen,,,    a hanakali taciro wayar daga cikin kwalinta, subahanAllah shine abun da tafurta lokacin  da'idanunta suka sauƙa akan haɗaɗɗiyar wayar, jikin wayar ma kaɗai abun kalloce balle kuma kakai ga shafata,  tabbas idan baza ta mantaba, wannan wayar itace wacce taji ƴan school ɗinsu na magana sabuwar fitowa ce, kuma burin kowanni  ɗan gata da ƴar gata, shine su mallaki wayar, domin kuwa aƙalla kuɗinta zaikai dubu ɗari biyar da tamanin,,  wani irin faɗuwar gaba taji ya shiga zuciyarta a lokaci guda,  take kuma mugun zargin Zaid ya ɗarsu acikin ranta, tabbas akwai abun daya ɓoye acikin zuciyarsa, amma idan ba haka ba babu yanda za'ayi yasiya mata wayan dubu ɗaruruwa, batare da suna da wani kyakkyawan alaƙa atsakaninsu ba,  a maimakon ta kunna wayar kamar yadda ya umarce ta, batayi hakan ba saima mai da wayar tayi cikin kwalinta haɗe da cusata cikin kayanta,  taƙudura acikin ranta cewa idan yasake da wowa zata mayar masa da wayarsa, domin ita bata kai martaba da ƙimar da zata riƙe wannan zuƙeƙiyar wayarba,,  sam bacci ya ƙaurace mawa idanun Zahrah  kalaman Zaid ne ketayi mata yawo acikin kunnu wanta,  bama kamar kalmar *INASONKI ZAHRAH* daya faɗa,  gaba ɗaya zuciyar Zahrah kasa sukuni tayi a wannan dare, da ƙyar bacci ɓarawo ya ɗauketa......

Zaid kuwa yana barin unguwar su Zahrah guest house ɗinsa ya nufa, sai dai yau ba ya tare da kowacce karuwa,   yana shiga cikin bedroom ɗinsa yasoma rage kayan jikinsa, saida yacire duk wani kaya dake jikinsa, kafun ya ɗaura towel a ƙugunsa kaitsaye ya  shige bathroom,,  a ƙalla ya kwashi kusan 1 hour a cikin bathroom ɗin kafun yafito, sanye da rigar wanka a jikinsa, gaban mirror ɗinsa yaje ya ɗanyi shafa,   combat jeans  black ya sanya haɗe da black t-shirt, sosai kyawun Zaid ya bayyana acikin wannan kayan, wayarsa kawai ya ɗauka yafice daga cikin ɗakin,  makeken friedge glass ɗin dake cikin katafaren falon nasa yanufa,  zuƙeƙiyar kwalbar

wine mai tsadar gaske yaɗauko a cikin friedge ɗin haɗe da glass cup zama yayi akan ɗaya daga cikin kujerun falon, yayinda ya buɗe kwalbar wine ɗin ya tsiyaya a cup, kana yakai bakinsa, a hankali yake shan wine ɗin, yayinda idanunsa ke alumshe, bakomai yake hasa sowa ba sai kyakkyawar surar Zahrah wacce ke tafiya da imaninsa ako da yaushe, haƙiƙa ya kamu da tsananin sha'awar Zahrah, kuma alƙawari yaɗaukar mawa kansa idan dai har yacika *SHU'UMIN NAMIJI* kamar yadda abokansa ke ƙiransa, to sai ya keta mawa Zahrah rigar mutumcinta kota wani hali kuwa,, wayarsa yaɗauka haɗe da lalubo numbern sim ɗin dake cikin wayar Zahrah, yana dialing aka sanar dashi cewa wayar a kashe take, wani irin munafukin murmushi Zaid yayi haɗe da sanya hanu ya shafi sajen dake kwance akan fuskarsa, kashe idanunsa ɗaya yayi haɗe da cewa "My Sugar Baby bakijin magana ko ?" yayi maganar tamkar wanda yake gabanta,, sosai Zaid ya sha wine a wannan dare, da ƙyar ma yasamu bacci ya ɗaukesa bayan yagama kwarara aman giyan da yasha .......

*21/October/2019*

*MRS SARDAUNA*

Copied By
YAYA HAYAT
(admin
Hayat hausa novels Group
Hausa novels and fashion Group
Cool novel, makeup and kitchen1 Group
And
WOMEN24 TV Group

WHATSAPP NO:+2349030159301